wanda ya yi haramar aikin hajji ko umara, sai

wani abokin gaba ya hana shi shiga ɗakin Allah, ko kuma wani haɗari ya same shi, ya kasa isa ɗakin Allah, to zai yanka hadayarsa a wurin da yake, sannan ya cire ihraminsa, saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki : {Idan an tsareku to abin da ya sauwaƙa daga hadaya}.[Al-baƙra :196].

Hadayar da ake yanka wa saboda tsarewa ita ce, Akuya ko raƙumi ko saniya.

## Wurin Da Ake Yanka Hadaya

Hadayar mai tamattu'i da ƙirani da ta sa kai, ana yanka ta a cikin iyakokin harami, a rabata ga miskinai, idan ya yanka ta a wajen iyakokin harami ba ta wadatar ba.

Hadayar tsarewa ana yanka ta a wurin da aka tsare mutum

## Lokacin Yanka Hadaya

### 1. Hadayar Mai Tamattu'i Da Kirani Da taɗauwa'i

Lokacinta yana farawa daga bayan sallar idi, ranar sallah, zuwa faɗuwa ranar ƙarshen kwanakin yanyana, ita ce ranar sha uku ga watan zul-hijja.

### 2. Hadayar Tsarewa

Lokacinta shi ne yayin da aka tsare mutum

> ## Lokacinta shi ne yayin da aka tsare mutum
>
> Kaɗan Daga Cikin Hukunce-Hukuncen Hadaya Da Layya
>
> Ya halatta Alhaji idan yana ƙirani ko tamattu'i ya wakilta wanda zai yanka masa hadaya, idan wakilin amintacce ne, amma abin da ya fi Alhaji ya yanka da kansa, saboda haka Annabi (S.A.W) ya aikata.
>
> Fansa bata wadatar wa daga layya, saboda ita fansa ana yin ta ne saboda tamattu'i, amma ita layya sunna ce ga Alhaji da waninsa.



https://www.al-feqh.com/ha